
# Dabarun Bincike

## (A Nazarin Harshe Da Adabi Da Al'adun Hausawa)



**Aliyu Muhammadu Bunza**

tetfund
TERTIARY EDUCATION TRUST FUND
Supported by Tertiary Education Trust Fund
TETFUND/DESS/UNI/GUSAU/AMB/14-15/01

Generated by CamScanner

# MARUBUCI

An haifi Aliyu a Unguwar Malamai Bunza 1962. Ya yi karatu Bunza Town Primary School 1969-1975, Government College Sokoto 1975-1980, University of Sokoto 1980-1985. Ya samu digirin MA BUK, 1989, PhD BUK, 1995. Yana da Diploma a Law da Arabic da Certificate in French. Ya wallafa littafan bincike 20. Ya fassara 12 (daga Turanci da Larabci zuwa Hausa) ya gabatar da takardu 164 a tarukan ilmi daban-daban daga ciki an wallafa 110 a mujallun ilmi. Ya duba kundayen bincike digiri (136) BA 77, MA 39 da PhD 20, ya jarraba digirin MA da PhD 13a waje. Yana da lambobin yabo 9 da kyaututtukan zama zakara 9. Ya samu kujerar Farfesa 2002 yana ɗan shekaru39, a lokacin shi ne ɗan autan Farfesoshin zamaninsa. Ya koyar a Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sokoto, Jami'ar Umaru Musa 'Yar'aduwa, Katsina, Jami'ar Jiha ta Nasarawa, Keffi, University of Cairo Egypt (2013), ya ci gajiyar Leventis Research Fellow (SOAS) University of London (1997) da Honorary Visiting Research Professor University College London (2006). Aliyu ya riƙe muƙamai 13 a cikin muƙaman jami'a. Aliyu na daga cikin ɗalibân da suka samu albarkar koyon karatu ƙarƙashin jigajigan karatun Hausa na farko Farfesa Muhammadu Hambali Junju, Farfesa M.K.M Galadanci, Farfesa Ɗalhatu Muhammad, Farfesa Ibrahim Yaro Yahaya, da wasu daga cikin manyan ɗalibansu. A yanzu (2017) Aliyu shi ne Madugun Tsangayar Fasaha da Ilmi kuma Shugaban Sashen Nazarin Harsuna da Al'adu, Jami'ar Tarayya Gusau.

# LITTAFI

Dabarun Bincike ɗan yunƙuri ne na gabatar wa ɗaliban ilmi fasahar bincike. Ya kalli bincike a matakan nazarin Hausa na Harshe, Adabi da Al'ada. An tsettsefe aikin cikin babuka 18. Babi na 1-8 sun tunkari share fagen bincike. Babi na 8-12 sun yi luguden manyan digirin Hausa da aka gabatar a jami'o'in Nijeriya da waje. Babi na 13-18 suka fuskanci yadda ake taskace bincike. Gaba ɗayan aikin a kan kundayen MA da Mphil da PhD da ba a wallafa ba kawai ya yi garkuwa. An ci nasarar gabato da taken kundayen manyan digiri ɗari tara da goma sha uku (913) na Hausa da waɗanda suka nazarci Bahaushe, da Kasar Hausa da gudummuwar Hausawa a fannonin rayuwar ɗan Adam; domin share wa mai bincike fagen nazari.

ISBN 978-978-959-419-1

9789789594191 06917

Printed by Ahmadu Bello University Press Ltd.,
P.M.B. 1094 Samaru, Zaria, Nigeria. Tel: 08065949711.
E-mail: abupresslimited2005@yahoo.co.uk;
Website: www.abupress.org

Generated by CamScanner